# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na biyar: A ƙarshen wasa, sai mu yi hannu da juna


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Mr. Madu | ɗan shekara 54 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan harkar wasan ƙwallon ƙafa a Afirka**.** Masu iya magana dai kan ce: "Wanda ya san sirrinka, shi ne mai tona ka". Zakari zai gane haka nan ba da jimawa ba. Amma ita kuma Safina fa? Za ta yanke shawarar zama ɗaya daga cikin waɗanda suka shiga gasar ne? Wane irin mataki antinta za ta ɗauka? Idan kuka kasance da mu, za ku ji duk amsoshin waɗannan tambayoyi. Kuma shirin na yau zai somo ne daga inda Zakari da Safina suka kama hanyarsu ta zuwa babban filin wasa.

**Fitowa ta 1: A babban filin wasa**

Zakari, Safina, John, Metogba, Shehu

**ZAKARI:** Safina, ni fa ina ganin wannan kamar ba shawara ba ce mai kyau.

**SAFINA:** Don Allah ka daina damun kanka! Ai ba wata matsala don mun je muna kallonsu? Kar ka damu! Za mu je ne kawai mu ga Metogba, da kuma ko su wane ne 'yan wasan, daga nan sai mu wuce. Ina hango su a tsakiyar filin.

**ZAKARI:** To shi ke nan. Bari mu je, ba kome!

**METOGBA:** Uhm, ga wasu makararrun nan zuwa. Na fahimci cewa ƙwarai akwai matsala sosai ta wajen ajiye lokaci.

**SHEHU:** Wai, yau na shiga uku! Yau abokantakata da Zaks ta ƙare!

**ZAKARI:** Wannan ba gaskiya ba ne! Wancan Shehu ne? … Kai kuma mayaudari ne! Yaya za a yi ka yi min haka? To, shi ke nan, yanzu zan koya maka hankali!

**METOGBA:** Kai! Kai, ku daina faɗan nan! Ku daina, na ce! Kai wane ne? Kuma wa ya ba ka izinin zuwa nan wurin, har ka fara yin faɗa da ɗaya daga cikin 'yan wasana?

**ZAKARI:** Wannan? Wannan? Ka yi haƙuri, *Coach*, amma ...

**SAFINA:** Bari in yi maka bayani, Metogba. Shehu da Zaks abokan juna ne. Wannan shi ne Zaks, kuma shi ne ya faɗa wa Shehu maganar wannan gasar da ake yi, bayan ya ji an faɗe ta a talabijin. Amma sai Shehu ya ce masa wai ɓata lokacinsu kawai za su yi, saboda an riga an gama zaɓen 'yan wasan da ake so. Saboda haka sai Zaks ya cire rai daga zuwa wurin gasar. Yanzu kuma da muka zo nan, wa za mu gani? Shehu!

**METOGBA:** Shehu, gaskiya ne?

**SHEHU:** E gaskiya ne, *Coach*. Na san cewa ba zan sami damar shiga ƙungiyar ba in dai har yana ciki. Me kuma zan yi? Rayuwa ce ta wanda ya fi wani ƙarfi kawai. Kowa ta kansa yake yi.

**ZAKARI:** Yaya za ka faɗi haka? Na yarda da kai, sannan kai babban abokina ne. Na ɗauke ka tamkar jinina.

**METOGBA:** To ya isa haka, bai kamata ku ɓata lokacinku ba, kuna faɗa sai ka ce dabbobi. Bari mu nemo mafita yanzun nan. Shehu, ka zaɓi wanda za ku yi wasa da su a gefe ɗaya. Zaks, kai ma haka, sannan mu yi wasa. Ni zan hura. Minti goma sha biyar ya isa.

**ZAKS:** Haka ya yi, *Coach*. Amma ina da buƙata ɗaya. Ina so Safina ta kasance a ɓangarena, da kuma ko da mata biyu ne da kuma wani namiji.

**JOHN:** Zaks, ni zan kasance a ɓangarenka.

**METOGBA:** Ya yi daidai! To kowa ya koma ɓangarensa, kuna da minti biyar ne kacal don ku shirya. Idan kuka ji na busa husur, ina so Zaks da Shehu, ku zo wuri na. An gane ko?

**DUKA:** E *Coach*, mun gane.

**MAI GABATARWA:**
Za a iya jin irin halin da waɗannan abokai biyu a da suke ciki, a yayin da suke ƙoƙarin haɗa ƙungiyoyinsu. A halin da ake ciki kuma a gidan Anti, wata mota ce mai tsada ta tsaya a ƙofar gidan. Gilasanta duk baƙaƙe, sannan Honourable Gambo na zaune a baya, yana yin waya a wayarsa ta salula.

**Fitowa ta 2: A waya**
Anti Lily, Honourable Gambo

**ANTI LILY:** Na'am, hallo? Lily ce. Wane ne wannan? Hallo?...Hallo?

**HON. GAMBO:** Lily? Ni ne Honourable Gambo. Kwana biyu, Lily.

**ANTI LILY:** Wane? Wa ya ba ka lambata? Kuma me kake so?

**HON. GAMBO:** Ko za mu iya haɗuwa, Lily? A gaskiya ma ina ƙofar gidanki ne yanzu haka.

**ANTI LILY:** A'a! Yanzu haka ma ba na gida. Bayan haka ma akwai 'yata da ke zaune da ni, saboda haka ba zai yiwu mu haɗu a gidana ba. Kana iya kirana wani lokaci. Sai an jima.

**HON.MAKEMBA:** Alo? Lily? Lily! … Direba, mu bar wurin nan don Allah.

**MAI GABATARWA**:

Lalle wannan kira na Honourable Gambo ba lafiya ba. Me yake nema a wurin Anti Lily wadda ma ga dukkan alamu ba ta gane shi ba? Bari mu manta da wannan. Anti Lily ta kama hanyar komawa gida cikin sauri, bayan ta tuna cewa ta bar 'yarta ita kaɗai a gidan. Sai dai ba ta san cewar Safina na can babban filin wasa ba. A filin wasan an fara karawa tsakanin 'yan ɓangaren Zakari da na Shehu.

**Fitowa ta 3: Wasan ƙwallon ƙafa tsakanin abokai biyu**

Zakari, Safina, John, Metogba, Shehu, Mr. Madu

**ZAKARI:** …ba ni nan…ba ni mana...bugo min ƙwallon! … Wash!

**METOGBA:** Mugun wasa! Bugun daga kai sai gola a ɓangaren Zakari! Kai kuma Shehu kana da *last warning*, idan ka ƙara wasa mara kyau, zan ba ka *red card*.

**ZAKARI:** Safina, ke nake so ki buga.

**SAFINA:** Ni? A'a! Me ya sa sai ni? Ai kai aka taɗiye.

**ZAKARI:** Za ki iya. Kin jefa min ƙwallo ɗazu da muka yi. Ki tsai da hankalinki a wuri ɗaya kawai.

**SAFINA:** Shi ke nan, bari in gwada.

**METOGBA:** Saura *second* hamsin, har yanzu ba ci. Zakari, ka tsai da wanda zai buga?

**SAFINA:** Ni ce zan buga.

**METOGBA:** *Goalkeeper*, ka shirya?

**SAFINA da 'YAN WASA:** *Oh Noooooo!*

**METOGBA:** Kwallo ta yi waje, kuma an kammala wasan a yau! To, kowa ya zo nan, kowa ya zo nan! Ku saurara ku ji! Kwallon ƙafa, wasa ne na ƙaunar juna, wasa ne na gina abokantaka mai ɗorewa tsakanin 'yan wasa, masu horad da su, 'yan kallo, da ma masu ɗaukar nauyin wasan. Gaskiya ne cewa za mu yi ta gardama da juna, har ma mu riƙa kiran juna da wasu irin sunaye marasa daɗi. Wani lokaci ma 'yan wasa har faɗa suke yi a fili, kamar yadda muka gani a yau. Amma idan an gama wasa, sai mu gaisa da juna. Saboda haka ina so in ga ku biyu kun gaisa da juna, wato Zakari da Shehu. ... Maza ku gaisa mana!

**'YAN WASA:** Ka yi daidai, *Coach*.

**METOGBA:** Shi ke nan, an kammala na yau. Sai kuma gobe in Allah ya kai mu da karfe takwas na safe. Af! Zaks, da kai da Safina, ina son zan yi wata magana da ku.

**'YAN WASA:** Shi ke nan, *Coach*, sai goben.

**ZAKARI:** *Coach*, ka yi haƙuri saboda halin da na nuna, na kasa daurewa ne.

**METOGBA:** Mu yi zaton cewa ha kan bai faru ba. Amma ba zan ƙara ɗaukar irin wannan halin ba nan gaba. *So*, kuna da sha'awar shiga gasar? Gaskiya ba zan ɓoye ba, Zakari, ka iya ƙwallon ƙafa yadda ya kamata, ke kuma Safina, wai! Ai bugun nan da kika yi sai ka ce wata ƙwararriya!

**SAFINA:** Ni? Ai ko ina da matuƙar buƙatar in shiga. Ina ciki!

**ZAKARI:** Ni ma haka.

**METOGBA:** Ya yi kyau, sai na gan ku goben ke nan. Barka dai, Mr. Madu!

**SAFINA da ZAKARI:** Barka da zuwa.

**MR. MADU:** Yauwa, barkanku dai.

**METOGBA:** Wannan shi ne Mr. Madu, shugaban ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasa. Don Allah ko za ka shirya motar da za ta mai da mu hotel ɗin?

**MR. MADU:** Ba damuwa. Ba wani abu kuma?

**METOGBA:** Ba wani abu, amma don Allah ka kira 'yar jaridar nan da ya yi hira da ni ɗazu, ta ƙara shirya wani taron 'yan jaridun.

**MR. MADU:** Wani kuma? Na mene ne?

**MAI GABATARWA**:
Tambaya mai kyau! Na mene ne? Me Metogba yake da shi da yake so jama'ar garin Gabas su ƙara ji? Za mu gano nan ba da daɗewa ba. Safina da Zakari, sun ji daɗi matuƙa da aka ba su damar shiga gasar zaɓen da ake yi. Bayan sun bar wurin wasan, sai Zaks ya kai ga shagon "Shah Electronics", don su kalli labarun wasanni, sannan ya nuna mata dukkan titunan dake garin Gabas. Duk a lokaci ɗaya, John, wanda suna tare da shi a filin wasan, shi kuma yana komawa gida tare da mahaifinshi, Honourable Gambo.

**Fitowa ta 4: A cikin motar Honourable Gambo**

Honourable Gambo, John

**HON. GAMBO:** Saboda haka, kana cewa Zakari, wanda ya fi kowa iya wasa a cikin ƙungiyar, kawai sai ya faɗa wa wani, har suka fara faɗa?

**JOHN:** Haka ne, Baba, amma yana da dalili kwakkwara. Ɗaya mutumin nan ne ya ci amanarsa a matsayinsa na babban abokinsa.

**HON. GAMBO:** Hmm, haka ne? To mene ne sunan abokin nashi?

**JOHN:** Sunansa Shehu. Su biyun duka gantali kawai suke yi a kan titi. Sannan kuma akwai wata yarinya.

**HON. GAMBO:** Shehu. *Okay*... Amma kar ka damu! Kai ne za a zaɓa a matsayin ɗan wasan da ya fi kowanne, wanda za a ɗauka!

**JOHN:** Wai, ai ban da tabbaci, Baba. Bayan irin yadda na ga Zakari na wasa da ƙwallon nan. Kai! Gaskiya, ban da tabbaci ko kaɗan.

**HON. GAMBO:** John, kai dai ka yarda da kanka da kuma ni mahaifinka. … *Driver*, kashe rediyon nan.

**MAI GABATARWA:**
Me kuma Honourable Gambo yake tunanin ƙullawa yanzu? A yayin da uba da ɗa suke hanyarsu ta zuwa gida, ita kuwa Safina da sabon abokinta Zakari, na hawa matattakalan gidan sama, wanda zai kai su ga gidan antin Safina ba tare da sanin me ke jiransu ba.

## Fitowa ta 5: A gidan Anti Lily

Safina, Zakari, Anti Lily

**SAFINA:** Wai, duk na gama gajiya kwata-kwata. Amma bari in gaya maka, gaskiya ina cike da farin ciki, wai a ce Metogba na gudanar da wajen gasa a garinmu! Wai wa zai taɓa tunanin haka zai faru?

**ZAKARI:** Ni ma na ji daɗi. Sai dai kawai, ban sani ba ko za mu ci gaba da abokantaka da Shehu? Kuma hakan ba zai yi daɗi ba saboda mun sha gwagwarmaya tare.

**SAFINA:** Ka ba da lokaci kawai. Wai! Allah ya kawo mu gida a ƙarshe. Wuuh!

**ANTI LILY:** Safina! Wai gidan wa kika je haka? Sannan kuma wane ne ya fasa min taga? Kuma..wane..ne..wannan, sannan wane...?

**SAFINA:** Anti! Lafiya kuwa? Kai, ina jin ba kya jin daɗi sosai. Zaks, don Allah ka taimaka min nan!

**ZAKARI:** To.

**MAI GABATARWA:**
Kafin Anti Lily ta gama tambayoyin da take yi, juwa ta ɗauke ta har ta kai ga faɗuwa. Me ya faru haka? Idan kuma ta farfaɗo, me za ta yi idan ta gane cewa Safina ta karya dokarta, har ta je ta buga ƙwallo? A can wurin gasar kuwa, al'amura sun fara yin zafi. Wa zai yi nasara? Wa zai faɗi? Sai ku kasance da mu a shiri na gaba don jin yadda za ta kaya. Idan kuma ana so a ƙara saurararon wannan shirin, sai a neme mu a adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.